| Umurnin SMS | Misalin Umurni/Rahoto (amfani da gajeren tsari idan akwai) |
|---|---|
| KAI RAHOTON KARIYA DA TSARO | |
| **SAURARA -** T22 zai kira ka ya kuma ba ka damar sauraran yankin da na'ura take. Yana buƙatar zaɓin T22 makarufo ta aikin Mai Reno. | **SAURARA,+123456789** |
| **Mataimakin Mutum -** Danna maɓallin tsoro sama da daƙiƙa 3 zai aika rahotanni guda 2 ga duk masu amfani. | Tramigo:an gano ƙararrawa,an kunna maɓallin tsoro, an faka, a Ofishin Tramigo, Bel Air, Birnin Makati, PH, 14.55895, 121.01931, 03:05 Okt 30 |
| Kira na Waya - Danna maɓallin waya sama da daƙiƙu 2 zai kira mai amfani na farko da yake cikin jerin bugun sauri. Danna maɓalli a karo na biyu zai kira mai amfani na 2 har zuwa masu amfani guda 3. Yi amfani da SD,1,lambarWaya don daɗa lamba zuwa rami 1. Umurnin SD zai jera masu amfani da ka saita. Domin amsa kira mai shigowa danna maɓallin waya. Ana buƙatar naúrar kai don yin amfani da wannan alama. | |
| KAI RAHOTON YIN AIKI DAIDAI | |
| **GUDU,x**<br>Zai yi rahoto idan mota tana tafiya sama da x km/h. Zango shi ne 10-300. Zai sake yin rahoto bayan mota ta ragae gudu 10km a da iyaka.<br>**GUDU,KASHE** kashe kai rahoto | **S,100**<br>**S,KASHE**<br>**Tramigo: An gano iyakar gudu 130 km/h, matsawa, 0.35 km Kudancin Harisson Plaza, Manila, NCR, RP, da gudu 121 km/h, 08:30 Nwb 2** |
| SAITAWA DA ADANI | |
| **SUNA,name -** Yana saita sunan motarka (har zuwa haruffa 15). Dole mai mai amfani ya kasance yana da iko na MAI ABU | **SUNA,Motar Gavin** |
| ƘARAMAIAMFANI,<lambar waya>,mataki - Yana ƙara maye gurabe a jerin mai amfani. Matakai zai iya zama MAI ABU, ABOKI, ko BAƘO<br>Mai abu zai iya bayar da dukkan umurnai, Baƙo NEMA kawai<br>JERAMAIAMFANIYana jera lambobi 4 na ƙarshe ga duk mai amfani<br>JERAMAIAMFANI,DUKYana jera ɗaukacin bayanan duk masu amfani<br>SHAREMAIAMFANI,XYana share takamaiman mai amfani<br>Dole mai amfani ya kasance yana da iko na MAI ABU. | AU,+5555555,MAI ABU<br>Yana ƙara lamba tare da ikon MAI AMFANI<br>JM<br>Tramigo: JeraMaiAmfani, 1-4556 2-5555, 22:58 Nwb 21<br>JM,DUK<br>Tramigo JeraMaiAmfani, #1 +5555555 Mai Abu - rahotanni: Wuta - Tafiya, 22:58 Nwb 21<br>SM,2 Yana share lambar mai amfani 2 |
| DAƊAWURI,wuri - Yana ƙara wurinka na kanka zuwa Kwatance wuri na Tramigo. Tramigo zai yi amfani da lura na wurin da abin hawarka yake a yanzu. Faki mafi kyau ka tsayar da abin hawanka da farko.<br>SHAREWURI,wuri<br>Yana cire wurin da ka daɗa ko wuri da aka ɗora da farko. Sunan wuri dole ya dace. | AP,Ofishi<br>Suna zai iya zuwa har lambobi 40. Manya da ƙananan baƙaƙe. Haruffa da lambobi kaɗai.<br>Yanzu gwada umurnin N:<br>Tramigo: an faja, a Ofishi, 20:38 Nwb 5<br>DP,Ofishi |
| **MATSAYI -** Yana yin rahoton matsayi na naúra da kuma rahotonnin da aka kunna maka. | **MT**<br>**Tramigo: matsayi, GPS: 60%, GSM: 80%, batur: 100%, rahotanni: Tafiya (15), Gudu (100), Shiyya (2.0, 14 33'31"N, 120 59'30"), 19:20 Nwb 7** |
| **SAITUNA -** Yana kai rahoton matsayi na dukkan rahoto na naúra da kuma adadin wuraren masu amfani da ka ƙara. Ga duk rahoto ana nuna lambar mai amfani | **SAITUNA**<br>Tramigo: Saituna, Ƙararrawa:-, Nema:-,Tayar da inji:-, Wuta.1, Tafiya:1/3/4, Gudu:-, Shiyya:1/2, wuraren mai amfani:2, Metric:kunna, 14:51 Nwb 7 |
| **LURA,KUNNA -** Yana ƙara lura da yanayin ƙasa ga duk wurare. LURA,DMS zai nuna tsarin yawan disimal. | **LURA,KUNNE**<br>Tramigo: an faka, 0.35 km Kudu da Harrison Plaza, Manila, NCR, RP, 14 33'34"N, 120 59'28"W, 11:33 Jnr 22 |
| **MABUƊI,tsohonMabuɗi,sabonMabuɗi** - Yana sauya mabuɗi na T22 ɗinka. Tsayin mabuɗi zai iya zama haruffa 20. Haruffa da lambobi kaɗai kuma ba mai bambancewa ne tsakanin manya da ƙananan baƙaƙe ba. | MABUƊI,0000,GAVIN123<br>Tramigo: Mabuɗi,an sauya zuwa GAVIN123, 11:33 Jan 22 |





## Magance Matsala

### Matsala ta 1: T22 ba ya amsawa.

Matsaloli da ka iya Haddasawa Ba wuta ko naúra tana barci
Hanyar Magancewa: Duba cewa akwai wuta a naúrar. Danjar naúrar za ta riƙa kiftawa bayan kowane daƙiƙu 5. Duba cewa an shigar da baturi daidai. Idan baturi ya yi ƙasa ka jona naúrar a wuta. Idan naúrar tana barci ne za ta tashi ta kuma amsa SMS ɗinka. Kira naúrar ka gani idan ka ji ringi duba matsala ta 3 idan ba ka ga matsala ta 2 ba.

### Matsala ta 2: Naúra ba ta amsawa kuma wutar GSM ta yi ja.

Matsaloli da ka iya Haddasawa: T22 ya kasa samun siginar GSM a wuri na yanzu, ba a shigar da SIM daidai ba; ba a sa SIM a naúrar ba, SIM yana da PIN da aka saita.
Hanyar Magancewa: Matsar da na'urar wurin da yake akwai sigina mai ƙarfi, Cire SIM ka sake shigar da SIM ɗin a naúrar, shigar da SIM a naúrar, cire lambar PIN ta SIM.

### Matsala ta 3: Naúra ba ta amsawa kuma siginar GSM tana walƙiya.

Matsaloli da ka iya Haddasawa: Babu kuɗi a SIM idan lissafi biya-baya ne, ko akwai matsalar hanyar sadarwa ta wucin gadi, ko lambar wayar mai amfani ba daidai take ba.
Hanyar Magancewa: Duba ka kuma tabbata akwai isassun kuɗi a cikin SIM, jira hanyar sadarwa ta dawo, duba lambar waya ta masu amfani.

### Matsala ta 4: Naúra ta yi rahoton tsohon wuri ko Ba kulle GPS kuma siginar GPS ja ce.

Matsaloli da ka iya haddasawa: T22 ya yi ruf-da-ciki, ba ya fuskantar sama, kusa da bishiyoyi, gidaje ko gine-gine da suke toshe siginar tauraron ɗan Adam, abin sa duhun gilashi na ƙarfe.
Hanyar Magancewa: Matsa zuwa wurin da T22 (tambarin Tramigo yake kallon sama) yake iya ganin sama sosai, tabbata abin sa duhun gilashi ba na ƙarfe ba ne. Domin gwada abin sa gilashi duhu, fitar da na'urar daga cikin abin hawa ka gani idan siginar GPS ta mutu a cikin minti xaya.

### Matsala ta 5: Na'ura ta yi rahoton baƙon wuri.

Matsaloli da ka iya haddasawa: Ba a ɗora Kwatancen Wuri na T22 ba.
Hanyar Magancewa: Tuntuɓi dillalinka ko goyon bayan Tramigo don smun Kwatancen Wuri na yankinka.

### Siginonin T22

Wuta - Tana filashi bayan kowane daƙiƙu 5, haske idan ana caji, mutuwa idan ana barci ko idan an kashe wuta
GSM - Kashewa yana nufin Ya yi, Kunnawa idan babu sigina, filasha idan babu matsala wajen aika SMS.
GPS - Kashe yana nufin Ya yi, Kunne idan babu wuri da aka ƙayyade.

### Yanayin Barci na T22

T22 yana da yanaye-yanayen sarrafa wuta guda 4 masu sarrafa kansu don tsawaita tsawon ran baturi ga masu amfani wajen ɗaukarsa a hannu da kuma kare zuƙewar baturin motarka ga masu amfani da suka shigar. A lokacin da take barci dukkan siginoni suna mutuwa don adana wuta.
T22 ɗinka za ta yi barcin awa 1 bayan tafiya ko bayan mintina 5 na rashin aiki. T22 tana farkawa a lokacin da aka fara tafiya, ko idan an gano motsi.
Yanayin Barci na Farko - Yana kashe GPS, ta farka na mintina 5 bayan kowane awa har tsawon awanni 6
Yanayin Barci na Biyu - Haka kuma yana kashe GSM saboda da haka sai ka jira na'urar ta farka domin amsa SMSɗinka. Yana kai kwanaki 5
Yanayin Barci na Uku - Yana tashi kullum har zuwa mintina 5. Yana zama har sai ƙarfin baturi ya zama ragu.
Yanayin Barci na Huɗu - Zai farka ne kawai idan an jona da wuta.
Idan har yanzu kana da mtsala tuntuɗi dillalinka ko aika imel support@tramigo.net domin neman taimako.



TRAMIGO™ T22

# Jagoran Mai Amfani

GA SIGAR FIRMWARE 1.40




## Mun gode maka da sayen Tramigo ɗinka naúrar bin sawu!

Wannan jagora zai taimaka maka ka saita T22 cikin sauri da kuma sauƙi. Idan kana da wasu tambayoyi tuntuɓi dillalinka ko ka aika saƙon imel zuwa support@tramigo.com. A kan Skype nema goyon baya na Tramigo domin nema ma'aikaci mai goyon baya da yake kan intanet. Duba www.tramigo.net don neman goyon bayan ɗaukakawa da kuma sababbin kayan haɗi na Tramigo.

### Matakan Shigarwa

1 ------------------- 2 -------------------- 3
Shigar Saitawa Bi

## Mataki na 1. Shigar

Idan an riga an shigar da T22 ɗinka tsallaka zuwa Mataki na 2 - Saitawa.




1. Yi cajin naúrarka na tsawon awanni 3 ta yin amfani da caja ta bango. Ka tabbata an sa baturi da kuma amfani da USB kebul domin yin haɗi da naúra zuwa caja sannan a danna maɓallin wuta na tsawon daƙika 2. A lokacin caji signar wuta za ta kasance a tsaye har sai an gama. Idan na'ura tana ma'ajiya zai ɗauki mintina 15 kafin siginar wuta ta kunnu.

Karin haske: Murfin baturi ba zai rufu ba idan ba a saka baturi daidai ba.

2. Kashe naúarar ka saka katin SIM. Bayan cajin naúra kana bukatar katin SIM saboda ka yi sadarwa tare da T22 ɗinka.

Tabbata cewa katin SIM ba shi da kariyar lambar PIN - za a yi wannan ta sa ka katin SIM a cikin wayar hannu da ta dace sannan ka bi umurni na cikin littafin wayarka don cire makul-lin PIN. Dole a saita lissafin SIM ɗinka don ba da damar SMS yin sako (rubutu) Za ka iya gwada SIM a wayar hannu don tabbatarwa zai aika SMS.


Cire marikin SIM.

Cire murfin batur ka kuma cire abin sa ka SIM kamar yadda aka nuna a hoton. Za ka iya amfani da biro wajen tura maɓalli mai launin rawaya sannan ka fito da marikin SIM. Sa ka SIM ɗina a cikin marikin ka kuma tura shi cikin naúrar.

Bayan ka shigar da SIM sannan ka tabbata ka shigar da baturi ka kuma kunna wutar naúrar. Siginar Wuta za ta rika filashi duk bayan daƙiku 5. Wutar GSM za ta zama ja na minti ɗaya kuma za ta mutu idan aka haɗa ta hanyar sadarwar GSM. Idan wutar ta zauna a jar ta duba ɓangaren matsaloli.

3. Zabi Wurin Naúra
Adaftan Wutar Kunna Taba da kuma USB kebul na T22
Ya danganta da yadda ka tsara yadda za ka yi amfani da Tramigo ɗinka waiwaya kan jagorori da suke kasa
Amfani na Ɗauka - Wutar baturi


T22 Adafta na Wutar Kunna Taba da kuma USB kebul.

Fito da naúrar waje har sai siginar GPS ta ɗauka - yanzu naúrar ta san wurinta. Ga jakunkunan ratayawa a baya da jakunkuna gwada saka naúrar a saman jakar da yake kallon sama. A jikin bel naúrar za ta yi aiki a gefensa, Ga abubuwan hawa za a saka naúrar a akwatin aajiye takardar gaba hannu, ko akwatin safa ko a matashi da yake bayan taga ta baya. Ga babura ko besfa saka a wajen ajiya - haka kuma za a iya saka wa a maɗauki domin kaucewa lalacewa.

Baturin zai kai kwanaki da yawa ya dogara da amfaninsa, saboda haka kunna kai rahoton Wuta (W,KUNNA) idan ka saita naúrar ta sanar da kai a lokacin da baturi ya bukaci caji. Yi amfani da caja ta bango kamar yadda za ka yi amfani a wayar hannu.

Amfani a Abun Hawa - Wutar Abin hawa
Fito da naúrar waje har sai siginar GPS ta ɗauke - yanzu naúrar ta san wurinta. Jona wayar wuta a





cikin wurin kunna taba, musamman wanda ake iya kunna shi ko da an kashe inji.

Dole a saka T22 tare da Tambari na Tramigo a sama yana kallon sama. Wannan don ya kyale T22 ta kayyade wurinta daga Dole a kaucewa kayayyaki kamar karfe, da abun sa gilashi duhu na karfe, da shitar taga ta baya saboda za su iya oshe waɗannan siginoni.

Idan ka ajiye mota a cikin gini ko a karkashin wani gini ba za la sami wuri ba har sai kana iya kallon sama.

Gaba ɗaya, za ka iya sa ran saka naúra a kan ko kusa da gaban abin hawanka zai zama mai gamsarwa. Za ka iya amfani da gam na yadi don adana T22 ɗinka a gaban mota. T22 zai yi aiki a cikin akwatin safar hannu, kwabar tsakiya ko ma a karkashin kujerar mai zaman banza da ake samu a akasarin abubuwan hawa,

Idan ka zaɓa wuri bar T22 a wurin na tsawon minti ɗaya ka kuma duba siginar GPS - za ta mutu idan T22 ta san wurinta. Idan siginar ta tsaya a launi ja duba ɓangaren magance matsala.

Haka kuma za ka iya amfani da eriyar GPS ta waje daban don zuwa wuri mai kyau a cikin abun hawarka.

Karin haske: Akwai nau'o'in abun sa gilashi duhu daga kamfanoni daban-daban da suke bayar da damar samun sigina ta lantarki ta ratsa.

## Mataki na 2. Saitawa

Bayan an saka T22 a cikin abin hawa ka shirya domin zama 'Mai Mallakar' T22 ɗinka. Masu mallaka ne kawai suke da cikakkiyar dama ga duk alamomi na Tramigo ɗinka Za ka yi sadarwa ne tare da T22 ta yin amfani da saƙonnin rubutu da aka aika a lambar wayar SIM ɗin da aka saka a T22 ɗinka Bi waɗannan matakai:

1) Aika SMS tare da sako MAI ABU,0000 zuwa T22 ɗinka. Idan T22 bai amsa ba je ka zuwa ɓangaren matsala. Lura 0000 ita ce lambar mabuɗi da kamfani ya saita da za ka iya sauyawa daga baya.

2) Bayan kimanin daƙiku 5-10 naúrar T22 za ta amsa tare da saƙon rubutu: "Tramigo: Mai abu,ba da amsa "Mai Abu, EE" don yin rijista a zaman mai abu"

3) Amsa da SMS tare da sako MAI ABU,EE zuwa ga T22 ɗinka

4) Bayan kamar daƙiku 5-10 anúrar T22 za ta amsa ta hanyar sakon rubutu: "Tramigo: Mai abu, +5551234578 an yi rijista, 09:25 Jan 14 Wannan yana nufin yanzu kai ne Mai T22 da aka yi wa rijista kuma zai karɓa duk wani umurni da ka aika zuwa gare shi daga wayrka.

5) Masarrafin Tramigo yana samar da mashiga mai saukin amfani da ta sa T22 ya zama mai saukin amfani a kan wayarka da kuma kwamfuta ɗinka. Akwai M1 a cikin faifan CD ɗinka na Tramigo ko ka duba www.tramigo.net domin sabuwar siga.

## Mataki na 3. Bi

Yanzu T22 ɗinka ya shirya don yin aiki. Daga kan wayarka ta hannu gwada aika umurnin NEMO zuwa ga naúrarka - kawai aika SMS ɗauke ta sako N a cikin saƙon - babba ko ƙaramin baƙi. Kunna tafiya da kuma kai rahoton wuta ta hanyar aika SMS ɗauke da T>W zuwa ga naúrar. T22 ɗinka zai amsa ta hanyar sako na tabbatar da cewa an kunna kai rahoto.

Domin kyale abokanka su nemo ka kara lambobin wayarsu ta yin amfani da umurnin DAƊAMAIAMFANI. Aika DM,lambarWaya,Aboki ya daɗa lambar aboki.

Gwada wsu daga cikin umurnai a takaitawa da ke kasa kuma ka haɗa motarka, babur, jirgin ruwa, ko jakarka ta baya!





## Umurnai na T22

Wannan ne jerin umurnai da za ka fi yin amfani da su. Domin samun cikakken jeri duba Jagoran Mai Amfani da T22 da yake kan faifan CD Tramigo ɗinka.

Aika ?, H ko Taimako don ganin jerin muhimman umurnai. Kowane mai amfani dole ya saita zaɓubɓukan kai rahoto na kansa saboda haka sai ka ba su dama ta yin amfani da umurnin DAƊAMAIAMFANI da aka jera a kasa.

Za a iya amfani da babba ko ƙaramin baƙi a umurnai. Mafi yawan umurnai suna gajeriyar hanya don rage yawan bugawa. Don rahotanni za ka iya kawai yin amfani da harafi ɗaya don kunna ko kashe rahoto. Misali aika sako da ya ƙunshi A zai kunna yin rahoton ƙararrawa idan yanzu haka yana kashe.
Umurnin SMS Misali Umurni/Rahoto (Amfani da gajerar hanya idan akwai)

| Umurnin SMS | Misalin Umurni/Rahoto (amfani da gajeren tsari idan akwai) |
|---|---|
| KAI RAHOTON WURI | |
| **NEMO -** Yana nuna wurin da motarka take. Haka kuma za ka iya aika saƙon SMS da ba komai a ciki<br>**NEMO,KUSA** yana nuna wurare 3 mafi kusa<br>**NEMO,time** yana kunna kai rahoto na lokaci-lokaci Za ka karɓi rahoton NEMO bayan kowane mintina x da aka keɓance tsakanin minti 1 da kuma mintina 1440 ko kullum ko mako-mako<br>**NEMO,kashe** yana kashe kai rahoto na lokaci-lokaci. | **N**<br>**N,KULLUM** zai aika rahoton NEMO sau ɗaya kullum<br>Tramigo:an faka, 0.58 km Gabas da Makati Sport Club/Salcedo Village, Makati, NCR, RP, tshon wuri, 20:38 Nwb 5<br>Naúra za ta nuna kamar yadda aka yi fakin har sai an fara tafiya<br>Rubutu tsohon wuri yana nufin cewa naúra ba ta ɗaukaka wuri ba sama da mintina 3 |
| **INA,wuri -** Yana nuna wurin da naúrarka take daga kowane wuri. Haka wuri da mai amfani ya ƙara yana aiki. Za ka yi amfani da yankin sunayen wurare kaɗan kuma naúra za ta zaɓa mafi kusa da suka dace. | **W,gida**<br><br>**Tramigo: an yi fakin, 5.18 km Arewacin Gida, 20:38 Nwb 5** |
| **TAFIYA,KUNNA -** Yana aika rahoto idan motarka ta fara tafiya da kuma bayan idan mota ta tsaya na mintina 15.<br>**TAFIYA,YANZU -** Zai yi rahoton tafiya da ake yi ko rahoton tafiya ta ƙarshe idan an faka naúra.<br>**TAFIYA,KASHE -** Yana kashe kai rahoton tafiya<br>**SAITA,FARATAFIYA,0 -** yana kashe kai rahoton fara tafiya | **T,KUNNA**<br>**T** Ba tare da faramitoci ba umurnin zai kunna kashe rahoto ko kunnawa.<br>**T,YANZU** Zai yi rahoton tafiya da ake yi ko rahoto na tafiya ta ƙarshe<br>**T,KASHE** Yana kashe kai rahoton tafiya |
| Tramigo: rahoton tafiya, fara 0.19 km Kudu da Titin Pasong Tamo-Dela Rosa, ƙare 0.02 km Kudu da Ofishin Tramigo, lokacin tafiya 0:27, nisa 1.61 km, iyakar gudu 33 km/h, matsakaicin gudu 3.5 km/h, lokacin tsayawa 0:07, 11:44 Nwb 6 | |
| **SHIYYA.nisa/kunna/kashe,sunaWuri -** Zai aika rahoto idan mota tana shiga ko tana barin wurin da aka ayyana ta zagayewa tare da ayyana radius ta nisa daga sunan wuri. Nisa zai kasance 0.1 km zuwa 999. Za ka yi amfani da yankin sunayen wurare kaɗan kuma naúra za ta zaɓa mafi kusa da suka dace.<br>**SHIYYA,KASHE -** Yana kashe kai rahoto | **S,1**<br>**S,3,GIDA**<br>**T22: an gano shiyyar ƙetarawa, motsawa 0:17 km NW daga Caltex, San Lorenzo, Birnin Makati, PH, E tare da gudu 34 km/h, 19:21 Jnr 27** |
| KAI RAHOTON KARIYA DA TSARO | |
| **ƘARARRAWA,KUNNA** - Zai yi rahoto idan naúra ta motsa ko an abin hawa ya matsa 100m. Dole ka sake kunna allo bayan kowace ƙararrawa.<br>**ƘARARRAWA,KASHE** - Yana kaseh allo. | **Ƙ,KUNNA**<br><br>**Tramigo: an gano ƙararrawar motsi, an ajiye a Glorietta Mall, Birnin Makati, PH, 17:07 Stm 15** |
| **WUTA,KUNNA -** Zai faɗa maka idan baturinka na T22 yana ƙasa da 20%.<br>**WUTA,KASHE -** Yana kashe allo. | **W,KUNNA**<br>**Tramigo: wuta kaɗan, an ajiye, 0:34 km Kudu da Harrison Plaza, Manila, NCR, RP 13:13 Okt 17** |